ISSN (print: ): 2141-3584 ISSN (online): 3121-7877
ZARIA JOURNAL OF LIBERAL ARTS
ZAJOLA
Journal of the Faculty of Arts
Ahmadu Bello University • Zaria • Nigeria
https://journals.abu.edu.ng/index.php/zajola Vol. 13, No. 1, June, 2025

# Kwatancin Al'adun Haihuwa Tsakanin Hausawa da Ga'anda

***Isa Umar AlMusawi***
Department of Arts Education (Hausa Unit),
School of Undergraduate Studies, Peacock College of Education, Jalingo.
isaumaralmusawi@gmail.com

## Abstract

*This study compares the birth traditions between the Hausa and Ga'anda communities in Gombi town of Adamawa state. The paper provides a summary of the history and the union of the two communities to compare the traditions of the birth between Hausa Muslims and Ga'anda Christians. Observation was used as a means of data collection during the birth ceremonies of the two communities. The results of this study shows that there are some customs that the Hausas do, but the Ga'anda do not do, such as: sharing of cow's leg and pepper soup among the relatives of woman who deliver (shan ƙauri), shaving the babies at the naming ceremony, slaughtering an animal for the babies and so on. There are other customs as well that the Ga'andas do, but the Hausas do not do them, they are: frequent taking of a sesame pap, preventing a patient with stomach ache from coming near the woman who delivers; so that she can not spread the disease to her, presence of women during the naming ceremony, choosing adoptive parents for the baby, in case something will happen to the parents of the baby later in life. Then there is the impact of the Hausa culture on Ga'anda, which includes: bathing the babies three times for a male child and four times for a female child, offering a feast to the woman who delivers the baby with the expectation of payment in the future, and gifts for the parents or the husband's family to the woman who deliver and so on.*

***Keywords****: birth, ceremony, culture, Hausa and Ga'anda.*

## Gabatarwa

Haihuwa ba don ke ba da iri ya ƙare inji masu hikimar magana. Haihuwa tana nufin samun ƙaruwa na ɗa namiji ko mace wadda hakan ke nuna ƙarin yawa a cikin zuriya. Al-Musawi (2023), ya dubi haihuwa da cewa ƙaruwa da ke sanya farin ciki ko akasin haka, ta hanyar fitar abin da ke ciki na ɗa ko wanin wannan zuwa nan duniyar. Bayan ya kai lokacin fitarsa ko a'a. Sannan bikin haihuwa kuwa yana farowa ne daga lokacin da mace ta sauka lafiya (Adamu, 2015). Ko-da-yake wasu suna ganin haihuwa da cewa mace ta ɗauki ciki na tsawon watanni

tara sannan ta yi naƙuda bayan zuban ruwan zaƙi, da fashewar faya sannan jariri ko jaririya ya faɗo, sannan uwa ko mahaifa ta biyo. Duk wannan yana faruwa ne bayan goyon ciki wanda mace kan yi (Muhammadu, 2020 da AlMusawi, 2023). Sannan an ƙara da cewa ciki ko junabiyu ko ɓatanwata duk kalmomi ne da Hausawa suke amfani da su domin bayyana wani hali da mata sukan shiga a sakamakon saduwarsu da ɗa namiji (Sallau, 2007).

## Manufar Bincike

Manufar wannan bincike ita ce yin kwatancin al'adun haihuwa tsakanin Hausawa Musulmai (saboda duk Hausawan da suke rayuwa a garin Gombi Musulmai ne) da Ga'anda Kiristoci (domin kashi saba'in daga cikin ɗari na Ga'anda Kiristoci ne) a Gombi, Jihar Adamawa**.** Ta hanyar zaƙulo kamancin da bambancin da ke tsakaninsu domin bayyanawa.

## Bayanin Maƙasudin Bincike

Kasancewar mai binciken yana da 'yar masaniya game da harshen Hausa da al'adunsa, kuma yana da zama a garin Gombi, yake da yaƙinin ba za a rasa kamanci da bambanci tsakanin al'adun haihuwar Hausawa da na Ga'anda ba.

## Sharhin Ayyukan Magabata

Akwai dalilai daban-daban waɗanda sukan sanya a buƙaci haihuwa, wannan kuwa yana faruwa ne bisa bambancin dalilan. Wurin wasu kuwa, buƙatar haihuwa ita ce saboda su samu mataimaka bayan sun gaji (tsufa). Ga wasu, buƙatar haihuwa tana zuwa ne domin samun magaji, bayan sun bar duniya (mutu). Yayin da wasu kuwa haihuwa jari ce, domin buƙatar tara iyali saboda samun majaya garma a cikin iyali, wanda hakan yake ƙarfafa tattalin arzikin zuriyar (Adamu, 1997 da Al-Musawi, 2023). Sannan, samun haihuwa ('ya'ya) yakan sanya farin ciki da annashuwa da ɗebe kewa da cire reni. Haka nan, daga cikin bukukuwa waɗanda Bahaushe yakan aiwatar akwai bikin samun ƙaruwa ta haihuwa. Biki wani taro ne da mutane ke shiryawa su gudanar domin nuna farin-ciki a kan wata baiwa da Allah ya yi wa waninsu, ko kuma don tunawa da wani abu muhimmi idan ranarsa ta zagayo. Bikin Hausawa ya faro ne daga gudummawa har ya koma bashi, musamman a tsakanin mata. Masana da manazarta al'adu sun yi ta musayar bayanai game da ma'anar wannan kalma ta 'biki' kamar: Kurfi (BSB), yana ganin biki a matsayin miƙa wani abu mai muhimmanci, kamar sandar girma, ko suna yayin da aka yi sabon haihuwa ko aure. Shi wannan masani, ya taƙaita bayaninsa kan miƙa wani abu mai muhimmanci ga wani, inda ya ba da misali da sandar girma da ake miƙa wa sarakuna bayan an naɗa su. Sai ya ƙara da taya wani murna

yayin da ya samu ƙaruwa ta haihuwa ko aure. CNHN (2006), ta bayyana biki da cewar shagali yana nuna farin-ciki wajen aure, ko suna ko naɗin sarauta ko salla ko al'adun gargajiya. Biki yana matsayin madubi ne ga al'umma domin yakan fito da zahirin hoton al'umma, wato yana bayyana al'adu da ɗabi'un al'umma baki ɗaya, tun daga addininsu da tufafinsu da abincinsu da wasanninsu da muhallinsu da sauran harkokinsu na rayuwar yau da kullum (Funtua, 2010). Lallai wannan masani, ya ɗebo ta da faɗi, domin wannan ma'anar da ya bai wa biki kusan ya taɓo rayuwar Bahaushe ne dukkanta.

Kowace al'umma tana da irin hanyoyin da take gudanar da bukukuwanta daban da wata al'ummar, wannan ya samo asali ne daga nau'in bikin da ake aiwatarwa wanda ya ƙunshi dalilin yinsa da lokacin yinsa da kuma muhimmancinsa, bugu da ƙari jama'a sukan tanadi mai kyau ga irin wannan bikin domin a yi shi cikin nasara, ba tare da an ji kunya ko nuna kasawa ba, wannan ne ya sa a wurin biki akan ci a sha gwargwadon iko. Tun kafin zuwan baƙi ƙasar Hausa, Hausawa mutane ne masu so da mutunta junansu.

**Taƙaitaccen Tarihin Hausawa**

Kalmar *Hausa*, kalma ce da take da gaɓa biyu watau '*Hau*' da '*Sa'*. Harshe ne na wata jama'a da ke rayuwa a kudancin hamadar Sahara (Al-Musawi, 2016). Dangane da bayanin wannan masani, Hausa harshe ne da wata al'umma take amfani da shi a matsayin hanyar sadarwa. Sannan CNHN (2006), ta ƙara bayyana Hausa da cewa harshen da Hausawa suke magana da mu'amala da shi, yana kuma cikin harsunan iyalan Cadi (Adamu, 1978 da Adamu, 1997 da CNHN, 1981 da kuma Gusau, 2012).

Harshen Hausa, harshe ne yalwatacce mai tarin hikimomi wurin isar da saƙo ta hanyar sassarƙa kalmomi. Saboda harshen ya wadatu da zantukan azanci kamar su: karin magana da zaurance da habaici da zuga da kirari da zambo da arashi da waskiya da gatse da gugar zana da sauransu (Ɗanhausa, 2012 da Ɗangambo, 2008 da Gusau, 2023 da kuma Kurfi, 2019). Yayin da ba lallai ne a samu wani harshe wanda ya ƙunshi waɗannan ba.

Wani masanin kuwa ya bayyana Hausa a matsayin ƙasa, da cewa an samo kalmar Hausa ne daga Buzaye, domin kuwa haka suke kiran mutanen da suke zaune a arewacin kogin Kwara, wato Hausa (Adamu, 1997). Kenan ƙasar da Hausawa suke rayuwa a doronta, ita ma sunanta Hausa a harshen Buzanci. Dangane da gurbin da ƙasar take kuwa, an bayyanata kamar haka:

> Makekiyar ƙasa da Hausawa suka mamaye su kaɗai, nan ciki kakanin kakaninsu suka tsira. Nan suka samu kansu, a nan aka same su. Ba su san wata ƙasa ba sai ita. Ba a san su a ko'ina ba, sai a nan. Ba su yi tarayya da kowa ba. Ba ga kowa suka karɓe ta ba, kuma babu wanda ya yi musu masauki a cikinta. Da ita suke tinƙaho, domin ba su san ko'ina ba bayanta. Da ita ake yi musu suna da garuruwansu da daulolinsu da zuri'arsu da addininsu da al'adunsu. A doronta suka kakkafa mazauninsu na din-din-din mannannu ƙuda ya faɗa ƙwaryar alewa. (Bunza, 2015).

An kwatanta wannan yanki (ƙasar Hausa), da cewa makekiyar ƙasa ce da take da manyan yankuna da kuma tsarin shugabanci a cikinta da cewa:

> …tana nan ne yamma da ƙasar Borno in ka fito daga (ƙasar) Yemen, tana da yankuna bakwai…a kowanne yanki akwai sarki, irin wannan sarki ɗayansu bai fi ɗaya ba, tsakatsakinsu ita ce Katsina, mafi yalwar ƙasarsu ita ce Zakzak (Zazzau), mafi faƙonsu ita ce Gobir, mafi yawan ruwansu ita ce Kano. Garuruwa ne ma'abota yashi da ƙoramu da duwatsu da kwarurruka da ruƙushi, baƙaƙen mutane (fata) ne ke rayuwa a wurin…(Fodiyo, 1383).

Lallai wannan masani ya fayyace taswirar ƙasar Hausa a fili na daga abin da ya shafi gurbi da yanayin ƙasa da yalwar yankuna, hatta matsayin shugabanninta sai da ya ambato. Bisa bayanansa ƙasar Hausa, ƙasa ce mai yabanya da dausayi, wanda hakan ya taimaka suke tasarrufi da ita wurin bunƙasa tattalin arziki. Ta fuskar abubuwan buƙatun ɗan Adam musamman abin da ya shafi abinci da muhalli da sutura da wanin waɗannan kuwa, yawan al'ummar Hausawa wanda ƙasar Hausa ta ƙunsa amsa ce ga mai neman ƙarin bayani. Saboda, yawan Hausawa ya ɗara mutum miliyan hamsin (www.joshuaproject.net/people-profile.php?peo3=12070&rog3=GH).

A al'ummance, Hausawa mutane ne masu riƙo da al'adunsu da suka gada tun iyaye da kakanni, musamman a kan abin da ya shafi sana'o'i da kasuwanci da cimaka da tufafi da shugabanci... Sannan, al'umma ce wanda take ƙuƙƙulla zumunci da dangantaka da ƙauna ta dukkan jinsunanta, a ko'ina suke a zazzaune (Gusau, 2021). Saboda haka, wannan ɗabi'ar ta yi tasiri ƙwarai da gaske a fagen gudanar da ayyukansu na yau da kullum.

Dangane da halayen Bahaushe kuwa an san shi da mutunci da karamci da haƙuri da zumunta da kawaici da riƙon addini da kamun kai da dattako da kama sana'a da juriya da jarumta da adalci da kunya da ladabi da biyayya da gaskiya… (Alhassan da wasu, 1982 da Kirk-Greene, 1974). Waɗannan masana sun fayyace kyawawan halayen Bahaushe, duk da cewa ba za a rasa bara-gurbi tsakaninsu ba, waɗanda suke aikata abin tir da assha. Domin akan samu masu mugayen halaye kamar ɓarayi da 'yan daudu da karuwai da wanin waɗannan daga cikin al'ummar Hausawa, kasancewar jama'a ta yi yawa, kuma in dambu ya yi yawa ba ya jin mai. Hakan ya faru ne dalilin haɗuwar Hausawa da wasu al'ummomin, ga kuma tasirin zamani.

**Taƙaitaccen Tarihin Ga'anda**

Ka'anda kamar yadda suke kiran kansu maimakon Ga'anda da Hausawa suke kiran su da shi. Yawanci Ga'anda ba su cika amfani da harafin /g/ ba, maimakonsa sukan yi amfani da harafin /k/ ne. Abin nufi al'ummar Ga'anda sukan musanya harafin /g/ da /k/ kasancewar harrufan biyu hanɗawa ne. Sababben abu ne musanya harafin /g/ da /k/… a harshen Ga'anda (AlMusawi, 2023 da Ibrahim, 2021).

Wurin da za a samu Ga'anda, ita ce farfajiyar nan da ta yi iyaka da ƙasar Kilba da Yungur da Bura da kuma Lala duk a cikin Jihar Adamawa. Chifartawa (2009), ya ce ƙabilar Ga'anda ta yi iyaka ne da ƙabilar Hona ta gabas da ƙabilar Lala ta yamma, sai ƙabilar Bura ta arewa da kuma ƙabilar Yungur ta kudancinta. Saboda haka tana nan a layi na goma ($10^0$N) a arewa da kuma layi na goma sha biyu ($12^0$E) gabas da ikwaita. A halin yanzu ƙasar (Gundumar) Ga'anda tana cikin Ƙaramar Hukumar Gombi ta Jihar Adamawa a Nijeriya.

Kamar kowace al'umma Ga'anda ma tana da hanyoyin da take bi domin raya tattalin arzikin da Allah ya hore mata, al'ummar Ga'anda mafi yawa daga cikinsu sun riƙi noma, domin samun abinci da kuma sayarwa sai 'yan kaɗan da suke kiwo da ƙira sai kuma sassaƙa saboda kayan aikin gona da kuma aikin gida. Girei (2011), ya ce Ga'anda sun fi noma abinci dangin dawa da shinkafa da wake, sai kuma riɗi da aya da ɗan abin da ba a rasa ba wanda ya ƙunshi gyaɗa da masara da sauran nau'in abinci wanda zamani ya kawo. Ƙabilar Ga'anda tana da al'adar aikin gayya musamman lokacin damina, inda ake haɗuwa a je gonar wannan in an nome ta sai koma ta wancan, hakan suke yi har damuna ta wuce, wannan tsarin aikin gayya shi suke cewa *MbohMbahta*. Sutura kuwa ƙabilar Ga'anda tana muhimmantar da wani zane da ake saƙawa *Kukwata,* duk da cewa ba a cika sayar

da shi ba. Girei (2011), ya bayyana cewa ana saƙa shi domin ɗaurawa sai kuma yi wa gawa sutura. Ko-da-yake yanzu zamani ya kawo tufafi nau'i dabandaban wanda hakan ya sanya tufafi ya wadata. Sannan ƙabilar Ga'anda tana bin addinin gargajiya ne wadda aka ce shi ne ma dalilin zuwanta muhallin da take a yanzu. Ibrahim (2021), ya ce tarihi ya nuna cewa sun nufo yamma ne bisa jagoranci wasu tukwane *Ngumgumi* da *Wanyidyerre*. Ita tukunyar *Ngumgummi* tana kare Ga'andawa ne daga yaƙi da kuma cututtuka yayin da tukunyar *Wanyidyerre* kuwa take samar da ruwan sama wanda za a sha a kuma yi amfani da shi lokacin damina. Duk waɗannan tukwane suna da mazauni ne a matsafar *Hurdufta* da ke kusa da unguwar *Gahumpa* da ke arewacin garin Ga'anda ta yau (AlMusawi, 2023). Kafin zuwan baƙi Ga'andawa suna bautar gumaka ne, Ga'andawa sun yi imanin cewa duk Baga'ande ransa yana nan ajiye a matsafar *Hurdufta*, saboda haka ne ma sukan ziyarci matsafar ga duk wani baƙon lamari da ya faru (Ibrahim, 2011). Sai dai zuwan baƙi da addinai ƙasar Ga'anda, ya haifar wa addinin gargajiya naƙasu wanda ya sa suka rungumi addini Kiristanci da kuma Musulunci, sai ɗan abin da ba a rasa ba na daga masu bin addinin gargajiya. Blench (2006), ya tabbatar da cewa kashi 70% na Ga'andawa Kiristoci ne, kashi 20% kuma Musulmi saura kashi 10% ne suke bin addinin gargajiya.

**Haɗuwar Hausawa da Ga'anda**

Sanin kowa ne Hausawa da yawansu 'yan kasuwa ne. Ado (2017), ya ce bincike ya tabbatar da cewa Hausawa suna da 'yan kasuwa masu yawa a cikinsu. Tun a zamanin da, sukan yi ciniki a tsakaninsu da sauran ƙasashe maƙwabtansu. Hakan ya sanya Hausawa suka ƙulla kyakkyawar alaƙa da al'ummar da suke hulɗar ciniki da su. Ana jin Hausawan farko da suka fara zuwa ƙasar Ga'anda 'yan koli ne, wannan kuwa ya faru ne wuraren shekarar 1938 (Al-Musawi, 2023). Sannan kasancewar ƙasar Ga'anda tana kan hanyar zuwa ƙasar Lala (Fotta) daga ƙasar Hona (Gombi), wannan ya sa akan samu Hausawa masu ya da zango kafin su wuce, ta hakan ma an samu sauƙin haɗuwar Hausawa da Ga'anda ta fuskar cinikayya. Daga baya kuma har ana samun Hausawa masu zuwa sayan amfanin gona (dawa da gyaɗa) da makamantansu. Su kuwa al'ummar Ga'anda sukan sayi tufafi da kayan masarufi dangin gishiri da sauransu a wurin Hausawan. AlMusawi (2023), ya ƙara da cewa wannan haɗuwar ta cinikayya ta haifar da yauƙaƙar dangantaka tsakanin al'ummomin biyu wanda har ta kai su ga auratayya da baranta da sauran lamuran da suka shafi zamantakewar rayuwa.

**Hanyoyin Tara Bayanai Domin Gudanar da Bincike**

An yi amfani da sanya idanu a matsayin hanyar tattara bayanai lokacin aiwatar da al'adun haihuwa, sannan an tattauna da masana al'adun na daga al'ummomin (Hausawa da Ga'anda).

**Kwatancin Al'adun Haihuwa Tsakanin Hausawa da Ga'anda**

A wannan gaɓar takardar ta kawo al'adun da ake aiwatarwa na haihuwa tsakanin al'ummar Hausawa da Ga'anda, sannan ta bayyana wurin da suke da kamanci da kuma wurin da suke da bambanci kamar haka:

**Sanar da Haihuwa**

A al'adar Hausawa, guɗa da shewa wanda mata kan yi bayan tsohuwa ta karɓi haihuwa suna daga cikin hanyoyin sanar da 'yan gida da maƙwabta cewa an sauka lafiya. Amma in a asibiti aka haihu *midwife* ko *nurse* ce ke karɓar haihuwar sannan su sanar.

A Ga'anda kuwa, tsohuwar da ta karɓi haihuwar ce za ta sanar da dangin maijego, su kuwa dangin maijego su sanar da haihuwar 'yarsu ga sauran al'umma. In kuwa a asibiti ne sai ma'aikatan jinya su sanar da haihuwar.

Kamanci tsakanin Hausawa da Ga'anda shi ne ana samun tsohuwa wadda ta saba da karɓar haihuwa (Ungozoma) ce take taimaka wa maijego wurin samu sauƙin haihuwa. Haka nan wani lokaci duk al'ummomin biyu suna haihuwa ne a asibiti.

Bambancin da ke tsakanin mai karɓar haihuwar Hausawa da Ga'anda shi ne, su Hausawa sukan iya gayyatar iyayen maijego su karɓi haihuwar, yayin da su kuwa Ga'anda iyayen maijego ba sa karɓar haihuwar 'yarsu. Sai dai wata mata daban ce za ta karɓi haihuwar.

**Binne Cibiya**

Cibiya ko mahaifa tana cikin wani ɓangare na jikin uwar jariri, saboda a jikinta jariri ya rayu har zuwa lokacin fitowarsa duniya. Bayan Ungozoma ta yanke cibi sannan ta wanke shi, sai ta nemi farin ƙyalle ta naɗe shi a ciki ta binne galibi a bayan ɗaki ake binnewa, sannan a kifa kasko a kanta a aladar Bahaushe.

A al'ummar Ga'anda lokacin da Ungozoma ta yanke cibi tana ɗaukarsa ne ta je bayan ɗaki ko wani wuri ƙuriyar gidan ta binne, sannan ta ɗora babban dutse a daidai kan ramin. Akan kuma yayyafa ruwan dumi a wurin da aka binne cibiyar taririn, domin kar ƙwari ko tsutsa su shiga cikin ramin.

Hausawa da Ga'anda sun haɗu kan binne cibiya da ake yi a bayan ɗaki ko wuri keɓantacce, sannan a ɗora wani abin a kai saboda shaida. Bambancin binne cibiyar Hausawa da na Ga'anda, su Hausawa sukan sanya cibiyar ne a cikin farin ƙyalle sannan su binne, su kuwa Ga'anda sukan binne shi ne ba tare da sanyawa cikin farin ƙyalle ba. Haka nan Hausawa sukan ɗora kasko ne daidai wurin da aka binne cibiyar, su kuwa Ga'anda sukan ɗora dutse ne a bisa wurin.

**Wankan Jariri**

Bayan jinin cibiya ya tsagaita ne Ungozoma za ta fara wanke jaririn da ruwan ɗumi tare da sabulun salo. Saboda in bai fita sosai ba, an ce daga wannan lokaci jaririn yake tasowa da warin ƙashi. Bisa al'ada, idan an gama wanka na farko, za a zubar da ruwan, sai mai zubarwar ta yi dariya, saboda jaririn ya taso mai fara'a, haka za ta yi sau uku in namiji ne, mace kuwa sau huɗu. Daga nan, za a riƙa yi wa jaririn nan wanka safe da yamma har na tsawon kwana arba'in har lokacin da maijego za ta yadawanka. Sannan, wannan ruwan da aka wanki jaririn da shi, za a riƙa zubawa ne a wurin da aka binne cibiyar, domin kar kiyashi su shiga cikin cibiyar. An ce in kiyashi suna shiga wurin cibiyar, jaririn zai riƙa yawan kuka wadda zai nuna alamar cikinsa yana ciwo. Haka abin yake a al'adar Hausawa.

Wankan jariri na farko a Ga'anda da ruwan ɗumi ne, in 'ya mace ce za a yi mata wanka sau huɗu, ɗa namiji kuwa sau uku. Sannan, Ungozoma ta riƙa ɗaga jaririn sama tana guntsan ruwan sanyi a bakinta tana fesa wa jaririn a gabansa sau uku saboda rigakafin kamuwa da gwaiwa. Sauran ruwan wankan jaririn za a riƙa zubawa a wurin da aka binne cibiyarsa, saboda, kar cikin jaririn ya riƙa ciwo.

Duk Hausawa da Ga'anda suna wankan jariri ne da ruwan ɗumi. Sannan, sukan yi wa jariri namiji wanka sau uku, mace kuwa sau huɗu, saboda riga-kafin kamuwa da warin ƙashi. Haka nan duk suna zuba sauran ruwan wankan jariri wurin da aka binne cibiyarsa, domin kare shi daga laulayin ciwon ciki.

Bambancin kuwa, su Hausawa mai wankan tana fara'a lokacin zubar da sauran ruwan wankan jariri saboda ya taso mai fara'a, yayin da Ga'anda kuwa ba su yin hakan. Su kuwa Ga'anda mai wankan jaririn bayan ta gama wankan za ta guntsi ruwan sanyi ta ɗaga jariri namiji ta fesa masa ruwan a gabansa, saboda rigakafin kamuwa da cutar gwaiwa, amma Hausawa ba su yin hakan.

**Gashin Cibi**

Gasa cibiya ke biyo bayan wankan jariri. Ungozomar Hausawa za ta sami kaskon da ya yi zafi ta riƙa ɗora tsumma yana ɗumi tana gasa cibiyar za ta faɗi cikin kwana uku ko huɗu, tare da gasa sauran jikin jariri musamman gaɓoɓi tare da jan hanci in mace ce domin ta yi karan hanci, da kuma luguiguita kai ga namiji. Daga nan kuma sai ta shafa masa mai wani lokaci akan shafe jariri da ɗanyen man shanu ko man kaɗe, sai dai yanzu akwai mayukan zamani kalakala da ake shafa wa yara, sannan, ta sanya masa tufafi.

Ungozomar Ga'anda za ta riƙa yin amfani da wani tsumma ko babban yatsanta na dama, saboda gasa cibin jaririn tare da sauran sassan jikinsa a shafa masa mai. Wasu daga cikin Ga'anda suna da al'adar cewa in cibiya ba ta faɗi cikin kwana uku ko huɗu ba, akwai matsala. Sai dai wasu suna ganin faɗuwar cibiyar jariri tsakanin kwanan uku zuwa huɗu, ya danganci zafin naman Ungozomar ne. In mace ce jaririyar akan haɗa da gashin kunne, ga wadda aka yi wa hujin kunne. Wasu kuwa man goge baki (*closeup)* suke shafawa a cibin domin ya warke da wuri.

Akwai kamanci tsakanin Hausawa da Ga'anda ta hanyar yin amfani da sanya tsumma a jikin kaskon wuta, in ya yi ɗumi, sannan a gasa jikin jaririn tare da shafe da mai. Haka ma wurin amincewa cibiya za ta faɗi a tsakanin tsawo kwanaki uku ga ɗa namiji ko huɗu ga ɗiya mace, a duk ɓangarorin biyu. Bambanci a lokacin gashin cibi, su Hausawa suna muhimmantar da jan hanci in mace ce domin ta yi karan hanci tare da luguiguita kai ga namiji, yayin da su kuwa Ga'anda ba su faye muhimmantar da hakan ba.

**Wankan Jego**

Wankan jego shi ne ake cewa wankan biƙi. Wanka ne na al'ada ga duk matar da ta haihu ko ta yi ɓari wurin Hausawa. Ruwa ake samu a haɗa shi da wasu saiwowi da sassaƙesassaƙe da ganyaye a cikin ƙatuwar tukunya ko garwa a banka masa wuta, ya tafasa sosai a zuba a cikin masaki ko bokiti sannan maijego ta yi wanka. Akan rage kaɗan saboda yi wa jariri wanka da shi. Akan samo ganyen maina ko runhu, wanda maijego za ta riƙa yafawa ko a yafa mata da shi (ga mai haihuwar farko). Ta hanyar tsoma ganyen cikin tafasasshen ruwan tana yarɓawa a jikinta har ruwan ya ƙare. Haka za ta riƙa yi safe da yamma har na tsawon kwana arba'in. Yin hakan yana maganin sammatsin sanyin haihuwa da kuma hana kumburin jiki, sannan wasu sukan bai wa maijego dauri har ma da jaririn. Ko-da-yake a yau zamani ya sanya wasu kan zuba *izal/septol* a cikin ruwan wankan domin kare ta

da kamuwa daga wasu cututtuka. Ga maijegon da ta ƙi bin wannan al'adar zai samar mata da matsalar rashin ƙarfin jiki da kumburi da sauran cututtukan haihuwa dabandaban. Wasu sukan yi wa maijego gargaɗi ta hanyar waƙa game da gujewa wankan jego kamar haka:

*Wankan jego maganin sumɓwita,*
*Yarinya daure ki yi shi ki huta,*
*In kin kuskure shi sai buzunki.*

(Hira da Azumi Umar)

Maijegon Ga'anda tana yin wanka ne na tsawon kwana uku ko huɗu, mafi tsawo na kwana bakwai da ruwan ɗumi. Sannan tana zama ne kan dutsen da aka binne cibiyar jaririnta lokacin wankan. Zamani ya yi tasiri a yau akan zuba *izal/septol* a cikin ruwan wankan maijego domin kare ta daga kamuwa da cututtuka. Hausawa da Ga'anda suna da kamanci a wankan jego kuma ruwan ɗumi suke amfani da shi na tsawon wasu kwanaki, saboda alkinta maijego tare da sama mata lafiyar jiki.

Su Hausawa suna haɗa ruwan wankan ne da wasu saiwowi da sassaƙesassaƙe da ganyaye a cikin ƙatuwar tukunya ko garwa a banka musu wuta, a dafa har su tafasa sosai a zuba shi cikin masaki ko bokiti maijego tana wanka da shi. Su kuwa Ga'anda suna wanka da ruwan ɗumi ne zalla ba tare da sanya wasu saiwowi ko saƙe-saƙi ba. Haka nan maijego a al'adar Hausawa tana wanka ne na tsawon kwana arba'in, su kuwa Ga'anda wankan kwana uku suke yi tsanani ba ya wuce na kwana bakwai.

**Barkar Haihuwa**

Barka wata al'ada ce mai muhmmanci tsakanin matan Hausawa, yawanci ana zuwa ne da dare domin a yi wa maijego murnar ta sauka lafiya. Bisa al'ada daga wannan zuwa barkatun ake fara karɓar biki, kowa zai ba da nasa bikin ne daidai gwargwadon ƙarfinsa ko kuwa ƙarfin bikin da ke tsakanin maijegon da wanda ta kawo. Irin kayakin da ake miƙawa sun haɗa da: kuɗi da suturar maijego ko jariri da sabulai da omo da turaruka da man shafawa da makamantansu.

Ga Ga'andawa ‘yan uwa da dangi sukan zo barka ne da ruwa a bokiti saboda maijego ba ta da ƙarfin zuwa ɗebo ruwa, kasancewar garin Ga'anda ana fama da matsalar ruwan sha. Kuma an fi zuwa barkan ne da safe ko yamma. Sai dai yanzu ana samun wasu sukan kawo wa maijego wani abin daban da ba ruwa ba, kamar su sabulu da omo saboda ta wanke kayan ƙarni. A al'adar Ga'anda duk mace mai ciwon ciki ba ta zuwa barkar haihuwa da wuri, sai bayan maijego ta kwana kamar huɗu zuwa mako guda da haihuwa, saboda ka da ta raɓa wa maijego ciwon

cikinta. In haihuwar kusa ce mai ciwon ciki za ta aiko wa maijego saƙon barkanta da haihuwa lafiya, sannan ta kuma sanar da cewa *ba zan samu damar zuwa yanzu ba sai nan gaba*, da haka ake gane cewa wance tana da ciwon ciki shi ya hana ta zuwa barkatu.

Kamar yadda Hausawa kan je barkar haihuwa haka su ma Ga'anda kan je wurin maijego domin taya ta murnar sauka lafiya. Haka nan an samu kamanci lokacin zuwan akan je da wani abin da zai taimaka wa maijego a sha'anin yau da kullum.

Lokacin da Hausawa kan je barkatu galiban da dare ne, su kuwa Ga'anda sukan je ne da safe ko da yamma. Haka nan su Hausawa kan je barkatu da kayan masarufi kamar sabulu da omo, su kuwa Ga'anda sukan muhimmantar da kai ruwa ne ga maijego. Haka nan matan Hausawa kan je barkatu ne babu wariya, yayin da matan Ga'anda duk mai ciwon ciki ba ta zuwa barkatu sai bayan wani lokaci, saboda ka da ta raɓa wa maijego ciwon cikinta.

**Shan Ƙauri**

Wata muhimmiyar al'ada ce a Hausada akan samo kaji ko kan akuya ko bindin saniya, ga mai ƙarfi har akuya ko tinkiya ake yankawa a haɗa da romo ana rabawa ga 'yan'uwa da abokan arziki, musamman ga waɗanda ba su samu kunun ƙauri ba. Hakan yana sake tunatar da cewa an samu ƙaruwa gidan wane, ko wance ta sauka lafiya kuma ranar kaza (a ambaci ranar) suna. Wasu sukan yi ƙauri a rana ta uku ko huɗu ko ma biyar daga ranar da aka yi haihuwar.

Ga'anda ba su da al'adar shan ƙauri.

**Raɗin Suna**

A ranar suna ana shimfiɗa tabarmi ne a ƙofar gidan da aka yi haihuwar ko kuwa a ƙofar babban gidan kakanin jaririn a zauna. Bayan yanka dabba da dawowar malami ƙofar gidan za a raba goro da minti ko cingam, sai maroƙi ya matso kusa da wurin zaman malamai tare da cewa "a saurara jama'a". Malamin zai bayyana sunan jariri ko jaririya sannan maroƙi zai ɗaga murya ya bayyana sunan saboda jama'a ta ji cewa wane aka samu (ya ambaci sunan jaririn). A kawo salatin Annabi goma ko sha ɗaya da niyar addu'ar raɗin suna. Sannan a yi ta jero addu'o'in neman albarka ga jariri da iyayensa da sauran addu'o'i masu alaƙa da hakan. A daidai wannan lokaci ne yara ƙanana za su shiga gida a guje suna waƙar a watso tare da ambatar sunan jaririn, kamar haka:

| ***Bayarwa*** | ***Amshi*** |
|---|---|
| *Ana fasa leda,* | *a watso* |
| *Musa aka samu,* | *a watso* |
| *ɗan albarka ne,* | *a watso* |
| *don Manzon Allah,* | *a watso* |
| *ko da minti ne,* | *a watso* |
| | (Hira da Malama Ladi Umaru) |

Ta wannan halin ne sauran matan da suke cikin gida ke sanin sunan da aka raɗa wa jariri, su kuwa matan sai su riƙa watso wa yaran minti da cingam ko dabino wani lokaci har da ʻyan kuɗaɗe. Sannan za a fitar da abinci iriiri ga mahalarta raɗin sunan domin su ci.
Bisa al'adar Ga'anda ana raɗa wa jariri sunan da iyaye suka zaɓa masa ne a cikin Coci. A wannan lokaci Pasto zai gayyaci iyayen juririn na haihuwa da kuma na riƙo (iyayen riƙo wasu mutane ne da iyayen jariri suka aminta da su, za su nema domin renon juririn ko da wani abu kamar mutuwar fuju'a za ta faru ga iyayen asali, to waɗannan iyayen riƙo ne za su reni juririn har ya kai shekara goma sha biyar) su zo gabansa domin raɗa wa juririn suna. Daga nan sai Pasto ya ce da jama'a su miƙe tsaye domin shaida raɗin sunan juririn, a nan Pasto zai ambaci sunan jariri kamar haka: *sunanka John!* Sannan sai a yi wa jariri baptisma kamar haka: *John (sunan juririn) ina yi maka baptisma da sunan uba da ɗa da kuma ruhu mai tsarki*, jama'a ku shaida. A wannan lokacin za a raba kayan ciyeciye da shayeshaye tare da raba goro da minti, saboda taya su murna.

Raɗa suna ga jariri yana yiwuwa ne daga malamin addini (liman ko pasto) kamanci ne hakan tsakanin Hausawa da Ga'anda. Haka nan ciyeciye da shaye-shaye tare da raba goro da minti da akan yi ga mahalarta wurin, nan ma an samu kamanci tsakanin waɗannan al'ummomi biyu.

Ga'anda sukan yi wa juririn suna ne tare da yi masa *baptisma* kasancewar yawancinsu Kiristoci ne, su kuwa Hausawa sunan kawai suke raɗawa babu baptisma kasancewarsu Musulmai. Haka nan cikin mahalarta wurin raɗin sunan Hausawa maroƙa da yara ƙanana suna da tasiri saboda su ne ke ɗaga sauti tare da sanar da abin da ke faruwa ga waɗanda ba sa kusa da mai magana (Liman), a ɗaya ɓangaren kuwa al'adar Ga'anda babu maroƙi su kuwa yara ba su da kataɓus a wurin. Sannan iyaye a Ga'anda sukan ɗauki jariri su kai shi Coci ranar suna su miƙa wa Pasto domin ya raɗa. Su kuwa Hausawa ko da masu raɗa suna a masallaci ne ba su kai juririn masallaci. Haka nan su Ga'anda sukan zaɓo wa jariri

iyayen riƙo ko da wani abu zai faru nan gaba ga iyayen asali, yayin da su kuwa Hausawa ba su da wannan al'adar. A al'adar Ga'anda maijego da sauran mata kan halarci wurin raɗin suna kasantuwar a Coci ake haɗuwa, su kuwa Hausawa maza ne zalla kan haɗu a wurin raɗin sunan. Sannan a wurin raɗin sunan Ga'anda Pasto kan umarci mahalarta su miƙe tsaye yayin da su kuwa Hausawa a zaune ake ƙare komai.

## Askin Suna

A aladar Hausawa, askin suna wanzami ne kan yi wa jariri ranar suna, bayan malamai da sauran maza manya sun raɗa suna sun tafi daga nan shi kuwa wanzami aikinsa zai fara, in dai ba wata matsala aka samu ga jariri tun lokacin haihuwa ba. Wanzami ne zai yi wa jariri askin farko bayan zuwansa duniya, za a kawo wa wanzami shimfiɗa kamar tabarma ya zauna sannan za a zo da jaririn a miƙa masa sai ya aske kan jaririn tas. Sannan ya tauna goron suna ya liƙa a daidai maɗigar jaririn maganin ciwon kai ko fashewarsa. Shi gashin kuwa sai ya cure shi wuri guda ya bai wa iyayen su yi wa jariri laya ko kuwa su kimanta nauyinsa su bai wa wanzami ladan aski. Wanzami yana aski, su kuwa mata a can cikin gida suna tara masa abin al'ada na daga kuɗi da sabulai da atamfa da sauransu. Baya ga aski wanzami yana cire beli da angurya ga jaririya da yin tsagar gado ko ta sana'a ga masu buƙatar hakan, sai dai zamani ya zo da wasu iyayen in ka cire aski babu abin da ake yi wa jariransu. Haka nan wasu kan sallami wanzami ne da kaya kamar hatsi da naman suna da tabarmar da yi wa jariri aski da zanin da aka saka jariri a ciki. Amma yanzu angon ƙauri (mahaifin jariri) kan sallami wanzami ne da kuɗi dai dai gwargwado, saboda halin yau.

Ga'anda ba su yi wa jariransu aski musamman ma mata, ko da yake wasu iyayen suna yi wa jaririnsu saisaye (barbing). Ga wasu iyayen sukan yi wa jariransu aski ne, idan ana haihuwa jariran suna mutuwa, daga nan in an haifi wani jaririn sai a yi masa aski ko kuwa kwale da zanen cibi, domin ya tsaya (ya rayu).

## Ya-Da-Wanka

Ya-da-wanka yana nufin kammala wankan jego wanda mai biƙi ta ɗebi tsawon kwana arba'in tana yi tun daga haihuwarta a al'adar Bahaushe. Yadawanka ne ke sanya a shiga neman sanin yadda ake tafiyar da renon yaro musamman ga haihuwar fari, musamman yadda ake ba shi nono da yi masa wanka da gane ma'anar kukansa na yunwa ko gajiya ko na rashin lafiya da sauransu. Maijego a al'adar Ga'anda tana yin wanka ne tsananinta na kwana bakwai. Sannan ta cigaba

da yin sha'aninta da koyon yadda ake kula da buƙatun jariri tare da sanin ma'anonin kukansa.

Waɗannan al'ummomin (Hausawa da Ga'anda) sun haɗu kan akwai wani miƙidarin lokacin da maijego za ta ɗauka tana wankan jego kafin ta yadawankan. Haka nan duk al'ummomin suna da kamanci wurin neman koyon sanin buƙatun jariransu.

Sai dai wurin da aka samu saɓani na cewa matan Hausawa suna ɗebe kwanaki arba'in ne suna wanka, su kuwa mata Ga'anda kwanakin da ba su wuce bakwai ba suke yi.

**Yawon Arba'in**

Yawon arba'in ziyara ce da maijego kan kai wa 'yan'uwa da abokan arziki bayan gama wankan jego a al'adar Bahaushe. Maijego kan goyi jariri ne da 'yar rakiya suke zaga gidaje, wani gidan in sun shiga su jima wani kuwa a tsaitsaye suke ziyarta su fice. Hakan za a zagaye gidajen waɗanda suka isa. A al'adance duk gidan da suka shiga za a bai wa maijego wani abun a ce an bai wa jaririn ne.

Ga'anda ba su da al'adar yawon arba'in.

**Garar Haihuwa**

Gara wata al'ada ce da iyaye kan kai wa 'ya'yansu kayan abinci zuwa gidan bikin suna ko aure. Saboda haka in maijego ta gama wanka, kuma dangin miji sun kawo kayan kome, to babu abin da iyayenta za su fara shirin yi sai haɗa mata kayan gara domin komawarta ɗakin mijinta. Kayan da ake haɗawa sun ƙunshi na abinci irin su: hatsi da kayan miya wasu har kayan ɗaki suke sauya wa maijego. Akan yi hakan ne gwargwadon ƙarfin iyayenta. Akan samu wasu iyayen ba su yi wa 'ya'yansu garar aure sai sun haihu ake haɗawa. Bayan tsayar da ranar dawowarta ɗaki, mijin zai tura danginsa da abin hawa domin ɗaukota.

Ga al'adar Ga'anda bayan maijego ta kammala iya kwanakin da mahaifiyarta ta alƙawarta za ta yi a gida, iyayenta sukan haɗo ta da kayan abinci irin su hatsi da gyaɗa da tsamiya da markaɗaɗɗen guna saboda yin kunu waɗanda za ta yi amfani da su bayan ta dawo ɗakin mijinta. Kamancin da ke akwai a tsakanin al'ummomin ita ce tanadar abinci daga iyayen maijego domin dawo da shi ɗakin mijinta, bayan zaman da ta yi a gidan iyayenta na koyon renon jaririnta sun cika.

Bambanci kuwa, su Hausawa lokacin da maijego za ta je goyon gida ba a sanya lokacin dawowarta sai daga baya iyayen miji ke zuwa domin neman dawowarta. Su kuwa Ga’anda sukan sanya ranar dawowarta ne tun lokacin da za ta koma goyon gida. Haka nan iyayen miji Hausawa ne sukan kai kayan komen haihuwa, su kuwa Ga’anda ba su kaiwa.

## Sakamakon Bincike

Wannan bincike mai taken Kwatancin Al'adun Haihuwa Tsakanin Hausawa da Ga’anda' an raba sakamakonsa zuwa kaso uku kamar yadda yake biye:

Akwai al’adun da Hausawa ke gudanarwa, amma Ga’anda ba su aiwatar da su. Waɗannan sun haɗa da: dafa kunun biƙi ga maijego da kuma raba shi ga maƙwabta da shan ƙauri ga maijego da raba wa wasu makusanta da askin suna ga jariri ranar suna da yanka dabba ga jaririn da aka haifa ranar suna da yawon arba’in da maijego za ta yi bayan ta gama wanka.

Sai wasu al’adu da Ga’anda suke gudanarwa, amma Hausawa ba su aiwatar da su. Waɗannan al’adun kuwa sun ƙunshi: yawaita shan kunun markaɗaɗɗen riɗi ga maijego, da rashin zuwan mai ciwon ciki barka a kan lokaci, saboda ka da ta raɓa wa maijego cutar, da halartar mata wurin raɗin suna, musamman maijego da jaririnta, da zaɓa wa jariri iyayen riƙo, ko da wani abu zai faru ga iyayen jariri (na asali), kafin jaririn ya girma.

Ga kuma tasirin da al’adun Hausawa suka yi wa na Ga’anda, waɗanda suka haɗa da: wankan jariri sau uku ga ɗa namiji da kuma sau huɗu ga ɗiya mace, da miƙa biki ga maijego tare da sanya tsammanin biya nan gaba, da kayan barka da iyaye ko dangin miji kan kai wa maijego, da taron mata gidan maijego ranar bikin sunan.

## Kammalawa

Wannan bincike wadda ya nazarcin kwatancin al'adun haihuwa tsakanin Hausawa da Ga'anda, an taƙaita shi ne daga lokacin da mace ta sauka lafiya da yadda za a sanar da haihuwar da binne cibiya da wankan jariri da gashin cibi da wankan jego da barkar haihuwa da shan ƙauri da raɗin suna da askin suna da yadawanka da yawon arba'in da garar haihuwa na al'ummomin Hausawa da kuma na Ga'anda, tare da kwatanta yadda suke aiwatar da su.

**Manazarta**


Adamu M. (1978). *The Hausa Factor in West African History*. Zaria: ABU Press Ltd.

Adamu, M. T. (1997*). Asalin Hausawa da Harshensu.* Kano: Ɗan Sarkin kura Publishers Ltd.

Adamu, M. T. (2015*). Haihuwa da Suna A Bahaushiyar Al'ada*. Kano: Salma-Aareef Publishers.

Ado, A. (2017). *Ra'o'in Bincike Kan Al'adun Hausawa.* Katsina: Kanki Classical Media Enterprises.

Alhassan, H. da wasu. (1982). *Zaman Hausawa*. Zaria: Northern Nigeria Publishing Company.

Al-Musawi, I. U. (2016). Teachers' Qualification and its Effect Towards the Academic Performance of Hausa Students in Some Selected Secondary Schools. (Unpublished B. A. Ed. Project). Bayero University, Kano.

AlMusawi, I. U. (2023). Kwatancin Wasu Bukukuwan Hausawa da na Ƙabilar Ga'anda. (Kundin Digiri na Biyu). Taraba State University, Jalingo.

Blench, R. (2006). *The AfroAsiantic Languages: Classification and Reference List*. https://en.wikipedia.org/wiki/Ga%27anda_language

Bunza, A. M. (2015, Yuni 15). Labarin Zuciya a Tambayi Fuska: Saƙon Dariya ga Sassanta Tsaro a Farfajiyar Karatun Hausa. (Makon Hausa) 2015. Jami'ar Ummaru Musa 'Yar 'aduwa, Katsina.

Chifartawa, P. A. (2009). *Topic in History of Ga'anda.* Yola: Parcelete Publishers.

CNHN. (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomas Nelson (Nigeria) Limited.

CNHN. (2006*).* K*amusun Hausa Na Jami'ar Bayero.* Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Ɗangambo, A. (2008). *Rabe-raben adabin Hausa*. Kaduna: Amana Publishers Limited.

Ɗanhausa, A. M. (2012). *Hausa mai dubun hikima*. Kano: Centuary research and publications company.

Fodiyo, M. B. U. (1383). *Infakul Maisur Fi Tareekhul Biladit Tukrur*. Alkahira: Daru wa Maɗabi'u Sha'ab.

Funtua, A. I. (2010). Bukukuwa. Gusau S. M. & Funtua, A. I. (Editoci) *Al'adu da Ɗabi'un Hausawa da Fulani (3693)*. Kaduna: El-Abbas Printer and Media Concept.

Girei, I. I. (2011). The Morphological Processes in Ga'anda Language. (Unpublished B. A. Project). University of Maiduguri, Maiduguri.

Gusau, G. U. (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: OlFaith Prints.

Gusau, S. M. (2021). *Tarihin wanzuwa da asalin Hausawa*. Kano: Commercial Printing and Publishing.

Gusau, S. M. (2023). Nazarin al'adu da adabi a al'ummar Hausawa a ƙasar Hausa a Arewacin Nijeriya. Takarda wadda aka gabatar a fadar mai martaba Sarkin Hausawan Turai a Paris, domin tunasarwa kan al'adu da adabin Hausawa da ƙarfafa tasirinsu da addinin Musulunci. Ranar Asabar Afirilu, 15, 2023.

https://www.joshuaproject.net/people-profile.php?peo3=12070&rog3=GH

Ibrahim, I. G. (2021). A Comporative Analysis of Some Features of Hausa And Ga'anda

Phonology. (Unpublished M. A. Dissertation). Taraba State University, Jalingo.

Kirk-Greene, A. H. M. (1974). *Mutumin kirki: The concept of the good man in Hausa*. Indiana: Indiana University Bloomington.

Kurfi, M. M. (2019). *Magana iyawa ce*. Katsina: Kanki Classical Media Venturers.

Kurfi, M. M. (BSB). *Kamusun Ingilishi da Hausa*. Katsina: Kanki Classical Media Enterprises.

Muhammad, M. M. (2005). *Adabin Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Muhammadu, M. S. (2020). *Bahaushiyar Al'ada.* Kano: Bayero University Press Limited.

Sallau, B. A. (2007). Ciki da Hanyoyin Tanadinsa a Tsakanin Hausawa a Yau. Takardara da aka Gabatar a Taron Ƙara wa Juna Ilmi na Ɗalibai Masu Karatun Digiri na uku (Ph.D) a Fannin Hausa, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

**Rataye**

**Jerin waɗanda aka yi hira da su**

| S/No | Suna | Shekaru | Aiki | Ranar Hira | Wurin Hira |
|---|---|---|---|---|---|
| 1. | Madam Nancy Nathan | 48 | Uwar maijego | 4/8/2023 | Unity Primary School Gombi. |
| 2. | Rev. Ayuba Ɗanjuma | 47 | Angon ƙauri | 6/8/2023 | Kusa da High Court Gombi. |
| 3. | Madam Victoria Jinas | 59 | Ungozoma | 9/8/2023 | Islamiya Pri. Sch, Gombi. |
| 4. | Namfiyan Alexander | 40 | Malamar jinya | 10/8/2023 | Gidanta a Dara Boddum, Gombi. |
| 5. | Ngata'alwa Kemson | 40 | Maijego | 11/8/2023 | A ɗakinta kwarwa, Gombi. |
| 6. | Samuel Karkumda | 57 | Pastor na LCCN | 13/8/2023 | Ung. Jeka da fari, Gombi. |
| 7. | Emmanuel Kakis Jones | 51 | Ma'aikacin Asibiti | 20/8/2023 | Shagon Tela Simon, Gombi. |
| 8. | Malama Ladi Umaru | 57 | Ungozoma | 21/8/2023 | Ung. Faransa, Gombi. |
| 9. | Malama Azumi Umar | 60 | Uwar maijego | 23/8/2023 | Tsamiyar kura, Gombi. |